

Da can mutane na zama da dabbobi.

Dabba ba ta kashe mutum.


Mutum ba ya kashe dabba.



A lokacin an yi wata yarinya.

Sunanta Ladi.

Ladi aikinta kitso ne.



Ana zaman lafiya a gari.


Dabbobi na harkarsu.

Mutane na harkarsu.

Sai wani zaki ya tada

zaune tsaye.






Zaki ya fara kashe

dabbobi.

Zaki ya fara kashe

mutane.

Gari ya ruɗe.


 

An kira taro a sasanta

da zaki.

Zaki ya ƙi zuwa taro.


An rasa na yi a gari.




Zaki yakan kitsa gashin fuskarsa.

Ladi ce mai yi wa zaki kitso.

Wata dabara ta zo wa Ladi.

Ranar kitson zaki ya
kewayo.
Ladi ta je kamar yanda
ta saba.
Zaki ya fito kitso a
ƙarƙashin bishiya.





Ladi ta kitsa gashin zaki

da igiya.

Ta ɗaure igiya a kan

bishiya.